**DOKOKI GOMA**

1. Kada ka kasance da wasu alloli sai Ni 2. Kada ka yiwa kanka wani Gunki 3. Kada ka kama sunan Ubangiji Allahnka a banza 4. Katuna da ranar asabaci 5. Ka girmama mahaifinka da mahaifiyarka 6. Kada kayi kisan kai 7. Kada kayi zina 8. Kada kayi sata 9. Ba za kayi karya ba 10. Kada kayi shaidar zur Gama zaka gamu da Ubangiji a ranar sharia. Yana ganin muguwar sha'awa a matsayin zina. Duk wanda ya kalli mace kallon sha'awa ya riga yayi zinar zuci da ita. (Matta 5:28) Ya kan ga kiyayya kamar kisa,"Dukan wanda ya ki wani dan'uwa ko yar'uwa shi mai kisan kai ne a zuci"(1Yohana 3:15) za kaje sama? Gawata gwadawa mai sauri, ko ka taba fadar karya, ka taba satar wani abu, ka taba fadar sunan Allah a banza, ko kataba yin kallo na sha'awa? Yakubu 2:10 tace, mutumin daya kiyaye dokoki duka amma ya karya daya, to ya karyasu duka kenan zaka zama mai laifi aramar sharia? Idan kayi wadannan abubuwa Allah yana ganinka a matsayin makaryaci, maiyin sata mai yin sabo mai yin zinar zuci. Littafi mai tsarki ya gaya mana cewa idan mutum yana da irin wadannan halaye karshensa shiga wutar jahanama. Allah ya aiko dansa domin ya sha wuya, ya kuma mutu akan gicciye. Yesu ya dauki hukunci akansa. Gama Allah yayi kaunar duniya har yaba da dansa haifaffe shi kadai domin dukan wanda yaba da gaskiya gareshi kada ya lalace, amma ya sami rai na har abada (Yohana 3;16) Yesu ya tashi daga matattu, yayi nasara da mutuwa. Ka tuba (kajuya gabarin zunubi) yau ka dogara ga yesu Almasihu. Allah kuwa zai baka rai na har abada ka karan ta littafi mai tsarki, kayi biyayya da abin da ka karanta.

**KALMAR ALLAH: I**

Kana bukatar ka somi ceto. Gaskiya nake gaya maka, ba zaka shiga mulkin Allah ba, idan ba an maye haifuwar kaba. (Yohana 3:3) Dukan mu muna kama da tumaki, kowa ya kama tafarkinsa. Mu rabu da hanyoyin Ubangiji muna bin namu hanyoyi. (Ishaya 53:6) Amma Ubangiji yana auna zuciya duka, yakuma gwada tunani naboye. Ya kuma ba kowa ladansa bisa ga abin da sukayi (Irmiya 17:10) zaku mutu, idan baku tuba daga zunuban ku, kun juyo ga Allah ba. (Luka 13:3). Bazaka iya ceton kan kaba. Allah ya cecemu ba domin kyawawan ayyukan muba, amma domin jinkansa. Ya wanke zunubanmu, ya bamu sabuwar haifuwa, da sabon hali, ta wurin Ruhu mai tsarki (Titus 3:5) Akwai hanyar da mutum yake tsammani daidaice amma karshenta hallaka (misalai 14:12) Yesu ya gaya masa cewa Nine hanya nine gaskiya, nine kuma rai, ba mai iya zuwa wurin Allah sai ta wurina (Yohana 14:6) Ba wanda zai iya gamsar Allah ta wurin sharia, tana iya gaya mana kawai mu masu zunubine. (Romawa 3:20) Allah ya tana da maka ceto. Yesu ya dauki zunubanmu a kan giciye don mu mutu ga zunubi, muyi abin da ke daidai. Ta wurin raunukan da akayi masa muka warke. (1Bitrus 2:24) yayin da kaba da gaskiya Allah zai ceceka ta wurin alherinsa. Ba za ka biya komai ba, wannan kyautace daga Allah. Ceto ba saboda kyawawan ayyuka bane da mukayi, kada kowa yayi faha riya (Afisawa 2:8-9)

**KALMAR ALLAH II**

Ka gaskata da Kalmar Allah ka sami tsira. Yesu ya gaya musu, "wannan shine kadai abin da Allah yake so daga gareku: ku gaskata da wanda ya aiko Ni" (Yohana 6:29) ina gaya muku gaskiya, duk wanda ya saurari sakon ya kuma gaskata da Allah wanda ya aikoni ya sami rai na har abada. Ba za'a hukunta su saboda zunuban su ba. Ga ma sun riga sun tserewa mutuwa sun kai ga rai madawwami. (Yohana 5:24) Duk wanda yake da Dan yana da rai; Wanda kuma bashi da Dan bashi da rai (1 Yohana 5:12-13) Ka shaida yesu a gaban mutane. Duk wanda yaji kunyar shaidani da sakona, Dan mutum ma zai ji kunyar wannan mutum (Luka 9:28) Idan ka shaida da bakinka cewa yesu Ubangijine ka kuma gaskata azuciyarka Allah ya ta shehi daga matattu zaka sami tsira. Ta wurin gaskatawa azucine zaka samu silhu da Allah. Ta wurin shaidawa da bakin ka zaka sami tsira. (Romawa 10;9-10) Bangaskiya ta kwarai tana haifarda kyawawan ayyuka . menene amfaninta idan kace kana da bangaskiya, amma baka nuna ta tawurin ayyukaba? (Yakubu 2:14) Gama Allah yana aiki a cikinka yana baka iko da marmari domin kayi abin da zai gamsheshi. (Filibiyawa 2;13) kowanne mutum zaiba da lissafin kansa a gaban Allah. (Romawa 14:12) Amma

idan kaki ka bautawa Ubangiji to sai ka zabi wandaza ka bautawa, amma ni da gidana zamu bauta wa Ubangiji (Joshuwa 24;15)

**SHIRIN ALLAH MAI SAUKI DOMIN CETO I**

Babbar tambaya acikin rayuwarka, itace kozaka je sama bayan kamutu? Allah yace, idan kana so kaje sama dolene amaya haifuwarka. (Yohana 3:7) A cikin littafi mai tsarki, Allah ya bayyana mana yadda za'a sake haifuwarmu. Dafarko, dolene ka gane cewa kai mai zunubine, Domin dukan mutane sunyi zunubine sun kasa kuma ga darajar Allah. (Romawa 3:23) Domin kai mai zununine don haka ka can can ci mutuwa. Saka makon zunubi mutuwane (Romawa 6:23) wannan ya hada da rabuwa ta har abada da Allah a Gidan wuta. An kadarawa ko wanne mutum ya mutu sau daya, Bayan wannan sai sharia. (Ibraniyawa 9:27) Amma Allah ya kauna ceka so sai har yaba da Dansa yesu, ya dauke zunuban mu ya kuma mutu a madadinmu. Amma Allah ya nuna mana kauna ta wurin aiko da Almasihu ya mutu amadadin mu tun muna masu zunubi (Romawa 5:8) ko dayake bazamu iya gane yadda Allah yaba da umarni ga kowa da kowa, kuma ako ina da su tuba su juyo zuwa gareshi (Ayy.M. 17:30) Tuba shine, kajuya daga zunubanka zuwa ga Allah, mutum yayarda shi mai zunubine, ya kuma yarda da abin da yesu yayi dominmu abisa gicciye. Tambayar itace menene zanyi domin in sami tsita? (Ayy.M. 16:30) amsar itace, ka yarda da yesu Almasihu wanda ya dauke zunubanmu, ya mutu a madadinmu, aka kuma bizneshi, amma Allah ya tasheshi. Ikon tashinsa daga matattu yabamu tabbacin samun rai na harabada yayin da muka tuba muka karbi yesu. Amma duka wadanda suka karbeshi, masu gaskatawa dashi yabasu ikon zama 'yayan Allah (Yohana 1:12)

**SHIRIN ALLAH MAI SAUKI NA SAMUN CETO**

Dukan wanda yayi kira bisa ga sunan Ubangiji zai tsira. (Romawa 10:13) kaba da gaskiya zaka sami tsira. Ikkilisiya ko aiki mai kyau ba zasu iya ceton kaba ba. Ka tuna Allahne kadai maiyin ceto. Shiri mai sauki na samin ceto shine. Kai mai zunubine, idan dai baka tuba ka karbi yesu wanda ya mutu domin kaba ba, to, zaka karasa sauran rayuwarka a cikin jahannama. Idan kaba da gaskiya gareshi a matsayin wanda aka gicciye dominka, aka bizne shi, yakuma tashi da rai, zai gafarta maka dukan zunubanka, ya kuma baka ceto na har abada ta wurin bangaskiya. Idan baka gane shirin sa da kyauba, kayi ta karanta wannan akai akai, har sai ka samu ganewa. Ranka yafi komai a duniyannan. Menene ribarka idan kasami dukan duniya abakin ranka? (Markus 8:36) ka tabbata ka sami ceto. Idan ka rasa ranka to ka rasa sama, ka kuma yi hasarar komai kenan. Kada ka dogara ga yadda kakeji, domin za'a iya samun canji.

Bayan da ka sami ceto akwai abubuwa guda uku da zaka rikayi domin kayi girma a cikin ruhabiya. Abu na farko shine kayi addu'a wannan shine lokacin da zakayi Magana da Allah. Na biyu shine ka karanta littafi maitsarki domin Allah yayi Magana da kai.

Abu na uku shine ka shaida bangaskiyarka ga wadansu, domin kayi Magana amadadin Allah. Kada kaji kunyar shaidawa wadansu labarin ceton Allahnka.

(II Tim 1:8) Duk wanda ya shaida ni anan duniya agaban mutane, nima zan shaidashi agaban Ubana a sama (Matta 1:32) Dolene ayi maka Baptisma, domin yin biyayya afili, daga nan saika hada kanka da ikkilisiyar dake koyar da maganar Allah.